NOOR
International

# SAƘONNIN RAYAYYUN NA ALƘUR'ANI:

## Kira ga Zukatan da ke Neman Gaskiya da waɗanda suka Yi Imani



noor.gallery

بسم الله الرحمن الرحيم

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jin qai




﴿ أَلَمۡ يَأۡنِ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن تَخۡشَعَ قُلُوبُهُمۡ لِذِكۡرِ ٱللَّهِ
وَمَا نَزَلَ مِنَ ٱلۡحَقِّ وَلَا يَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلۡكِتَٰبَ مِن قَبۡلُ فَطَالَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَمَدُ فَقَسَتۡ
قُلُوبُهُمۡۖ وَكَثِيرٞ مِّنۡهُمۡ فَٰسِقُونَ ١٦ ﴾
[الحديد:١٦]

*Yanzu lokaci bai yi ba ga waxanda suka yi imani zukatansu su yi taushi da zikirin Allah da kuma abin da Ya saukar na gaskiya, kuma kada su zama kamar waxanda aka bai wa Littafi tun gabaninsu, sai lokaci ya tsawaita a gare su, sai zukatansu suka qeqashe; mafiya yawa kuma daga cikinsu fasiqai ne?*

**Alkur'ani** (57:16)

AIKON DIN AIKI - TONA

NOOR
International



﴿ٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَۖ
إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۗ وَلَذِكۡرُ
ٱللَّهِ أَكۡبَرُۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تَصۡنَعُونَ ٤٥﴾

[ العنكبوت: ٤٥]

*Ka karanta abin da ake yi maka wahayinsa na Alqur'ani, ka kuma tsai da salla; lalle salla tana hana alfasha da kuma abin qi. Kuma tabbas ambaton Allah shi ne mafi girma. Kuma Allah Yana sane da abin da kuke aikatawa*

**Alkur'ani** (29:45)

AIKON DIN AIKI - TONA



NOOR
International

﴿ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ مُبَٰرَكٞ لِّيَدَّبَّرُوٓاْ
ءَايَٰتِهِۦ وَلِيَتَذَكَّرَ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢٩ ﴾

[ص: ٢٩]

*Littafi ne mai albarka da Muka saukar maka da shi domin su yi tuntuntuni game da ayoyinsa, don kuma masu hankula su wa'azantu*

**Alkur'ani** (38:29)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿وَلَنَبۡلُوَنَّكُم بِشَيۡءٖ مِّنَ ٱلۡخَوۡفِ وَٱلۡجُوعِ
وَنَقۡصٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡوَٰلِ وَٱلۡأَنفُسِ وَٱلثَّمَرَٰتِۗ
وَبَشِّرِ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٥﴾

[البقرة:١٥٥]

*Kuma lalle za Mu jarrabe ku da wani abin tsoro da yunwa da tawayar dukiya da ta rayuka da ta ‘ya’yan itatuwa. Don haka ka yi albishir ga masu haquri*

**Alkur'ani** (2:155)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱسۡتَعِينُواْ بِٱلصَّبۡرِ وَٱلصَّلَوٰةِۚ
إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٥٣﴾

[البقرة:١٥٣]

*Ya ku waxanda suka yi imani ku nemi taimako ta hanyar haquri da salla. Lalle Allah Yana tare da masu haquri*

**Alkur'ani** (2: 153)

AIKON DIN AIKI - TONA

NOOR
International




﴿ٱلَّذِينَ إِذَآ أَصَٰبَتۡهُم مُّصِيبَةٞ قَالُوٓاْ إِنَّا لِلَّهِ وَإِنَّآ
إِلَيۡهِ رَٰجِعُونَ ١٥٦﴾

[البقرة:١٥٦]

*(Su ne) waxanda idan wata musiba ta same su sai su ce: "Lalle mu na Allah ne, kuma lalle mu gare Shi muke komawa."*

**Alkur'ani** (2:156)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿ ٱلرَّحۡمَٰنُ ١٠ عَلَّمَ ٱلۡقُرۡءَانَ ١١ خَلَقَ
ٱلۡإِنسَٰنَ ١٢ عَلَّمَهُ ٱلۡبَيَانَ ١٣ ﴾

[الرحمن ١-٤]

*(Allah) Mai rahama Shi Ya koyar da Alqur'ani Ya halicci mutum Ya koyar da shi bayani*

**Alkur'ani** (55: 1- 4)

AIKON DIN AIKI - TONA



NOOR
International

﴿أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلۡقُرۡءَانَ أَمۡ عَلَىٰ قُلُوبٍ
أَقۡفَالُهَآ ٢٤﴾

[محمد: ٢٤]

*Yanzu ba za su yi tunani na basira ba (game da) Alqur'ani ba, ko kuwa akwai wani rufi ne a kan zukatansu?*

**Alkur'ani** (47: 24)

AIKON DIN AIKI - TONA



NOOR
International

﴿إِنَّ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانَ يَهْدِى لِلَّتِى هِىَ أَقْوَمُ
وَيُبَشِّرُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعْمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
أَنَّ لَهُمْ أَجْرًا كَبِيرًا ٩﴾

[الاسراء: ٩]

*Lalle wannan Alqur'anin yana shiryarwa ne ga (hanya) mafi miqewa, yana kuma yi wa muminai waxanda suke yin kyawawan ayyuka albishir cewa, lalle suna da lada mai girma*

**Alkur'ani** (17:9)

AIKON DIN AIKI - TONA




﴿وَلَوۡ جَعَلۡنَٰهُ قُرۡءَانًا أَعۡجَمِيّٗا لَّقَالُواْ لَوۡلَا فُصِّلَتۡ ءَايَٰتُهُۥٓۖ
ءَا۬عۡجَمِيّٞ وَعَرَبِيّٞۗ قُلۡ هُوَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ هُدٗى وَشِفَآءٞۚ وَٱلَّذِينَ لَا
يُؤۡمِنُونَ فِيٓ ءَاذَانِهِمۡ وَقۡرٞ وَهُوَ عَلَيۡهِمۡ عَمًىۚ أُوْلَٰٓئِكَ يُنَادَوۡنَ
مِن مَّكَانِۭ بَعِيدٖ ٤٤﴾

[فصّلت: ٤٤]

*Da Mun sanya shi Alqur'ani Ba'ajame da tabbas za su ce: "Me ya hana a bayyana ayoyinsa? Yanzu (a ce Alqur'ani) Ba'ajame (Annabi kuma) Balarabe?" Ka ce: "Shi ga waxanda suka yi imani shiriya ne da waraka. Waxanda kuwa ba sa yin imani akwai nauyi cikin kunnuwansu, shi kuma makanta ne a gare su." Waxannan (sun yi kama da waxanda) ake kira daga wuri mai nisa*

**Alkur'ani** (41: 44)

AIKON DIN AIKI - TONA